# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Kowa dabam Allah ya yi shi: Mutunta haƙƙin tsirarru
## Kashi na tara: Labarin Aminata – bazawarar da mijinta ya mutu a ƙasar Senegal

Wanda ya rubuta: Babou Diallo
Wanda ya fassara: Ɗanlami Bala Gwammaja
Wadda ta tace: Halima C. Schmaling

**'Yan Wasa:**

Mai ba da labari

| | |
|---|---|
| Aminata: | 'yar shekara 25 |
| Mamadou Dabo: | ɗan shekara 35 |
| Hélène: | 'yar shekara 30 |
| Idrissa Konaté: | ɗan shekara 41 |
| Aliou Fofana: | ɗan shekara 37 |

**Mai gabatarwa:**

Jama'a, barkanmu da sake saduwa da ku a kashi na tara cikin shirinmu na "Ji Ka Karu" mai suna "Kowa Dabam Allah Ya Yi Shi – Mutunta Haƙƙin Tsirarru". A yau za mu tattauna ne a kan irin matan nan da mazajensu suka mutu suka bar su a nahiyarmu ta Afirka, musamman ma a ƙasar Senegal.

Matan da aka mutu aka bari wani rukunin tsirarrun mutane ne da wani lokaci suke samun kansu a halin gudanar da rayuwar kaɗaici. A ƙasar Senegal, yawanci sukan yi rayuwa mai wahala kamar dai yadda abin yake a sauran sassan Afirka. Ɗawainiyar kula da ilimin 'ya'yansu, da ciyar da su, da kuma samar musu muhalli, waɗannan na daga cikin matsalolin da suke zama musu ƙalubale a rayuwarsu ta yau da kullum. Ba wani sabon abu ba ne iyayensu da dangin mazajensu, har ma da sauran al'umma su ƙi tallafa musu. Wannan shi ne abin da ya faru ga Aminata, wadda ta rasa mijinta shekaru biyu da suka gabata. Bayanin da ta yi ya nuna yadda rayuwa take tsananta ga mafi yawan matan da aka mutu aka bari a Senegal.

**Mai ba da labari:**

Ga dai wata mata matashiya nan siririya baƙa, tana sanye da doguwar riga ta atamfa, zaune a kan doguwar kujera tana waya, ta kuma kura wa talabijin ido. Haka Aminata takan yi kowace yamma.

Yanzu ƙarfe shida ne na yamma, garin kuma akwai ɗan sanyi-sanyi. Ga dai ita wannan mata Aminata nan kamar tana kan ganiyarta, amma ita ce take ɗaukar ɗawainyar 'ya'yanta mata guda biyu, 'yar shekara goma da 'yar shekara takwas, sai kuma namiji ɗaya dan shekara shida, suna kuma zaune ne a Niarry Tally, wata unguwa da take a wata gundumar Dakar mai cike da mutane.

**Bayanin Aminata cikin Faransanci:**

*"Tun lokacin da mijina ya rasu kamfanin da yake yi wa aiki ne suke kula da ni. Ina karɓar albashinsa duk wata saboda ya rasu ne kafin lokacin barin aikinsa. Wannan shi ne kuɗin da nake amfani shi wajen biyan kuɗin haya da kuɗin ruwa da na wuta da kuma ɗawainiyar yara."*

**Mai ba da labari:**

Kuɗin CFA 75,000 ne, kimanin Yuro 115. Wannan shi ne ɗan kuɗin fanshon da yake samu. Amma duk da haka Aminata na ɗaya daga cikin matan da suka yi sa'a. Akwai matan da aka mutu aka bari da dama da za su so a ce sun samu ya tata. Ba ko da yaushe ake ba wa matan ma'aikatan da suka mutu irin wannan taimakon kuɗi ba. Idan ma har ana ba su ɗin, to a yawancin ƙasashen Afirka abin da ake ba su bai taka kara ya karya ba, kuma sau uku ake ba su a shekara, sannan ba ya wuce CFA 30,000 zuwa 45,000 ba, wato Yurot 50 zuwa 70 kacal.

Aminata ta ɗanɗana rayuwa mai daɗi. Mijinta ya yi iyakar ƙoƙarinsa wajen ganin ta samu rayuwa mai kyau. Misali ya sha ba ta kayayyaki kamar shaddodi da atamfofi. Har yanzu ba ta manta da irin wannan yanayin ba kamar yadda ba ta manta da ranar da mijin nata ya mutu ba. Oumar ya rasa ransa ne a haɗarin mota a kan hanyarsa ta komawa gida daga wurin aiki. Shekarunsa 28. Duk da halin juyayi da Aminata ta samun kanta a ciki ba ta taɓa karaya ba:

**Bayanin Aminata cikin Faransanci:**

*"Duk lokacin da nake fuskantar wata matsalar rayuwa sai na roƙi Allah Ya taimake ni, na kuma tashi tsaye a kai. Ina kuma la'akari da abin da zai je ya zo."*

**Mai ba da labari:**

Duk lokacin da ta ji wannan kiɗa na rap da Maxi Crazy ya yi, sai ta sami ƙarfin jiki. Saƙon da wannan mawaƙin ɗan ƙasar Senegal yake isarwa abu ne mai sauƙi: rayuwa kamar yaƙi ce, kada ka karaya. Yawancin matan da aka mutu aka bari sun san abin da ake nufi da wannan. Dangin mazajensu sukan yi watsi da su, su kuma rasa duk wata hanya ta samun tallafi wanda wannan yakan sa su rasa yadda za su yi. Ya kuma zame musu dole su ci gaba da ɗawainiyar rayuwar yau da kullum, su ciyar da kansu, su tufatar da kansu, su kuma kula da yara da dai sauransu. A irin wannan hali, dole ne sai sun nutsu kamar yadda Aminata take yi. Tana kuma shawartar sauran matan da aka

mutu aka bari da su yi koyi da ita.

**Bayanin Aminata cikin Faransanci:**

*"Ina faɗa musu yadda nakan yi na samu mafita. Sukan tambaye ni ko ina samun tallafi daga wajen surukaina, ni kuma nakan ce musu a'a. Ina amfani ne da albashin da mijina ya bar mana. Da su nake amfani wajen kula da yara da ma sauran harkokin rayuwa. Amma ina juya ɗan wani abu daga ciki na ajiye ribar da nakan samu. Don haka ba na ɓarnatar da kuɗi, saboda akwai yara a gabana da nake kula da su. Dole ne na yi abin da ubansu yake yi musu. Wannan ita ce shawarar da nake ba wa ƙawayena, matan da aka mutu aka bari. Akwai waɗanda suke amfani da ita kuma."*

**Mai ba da labari:**

Aminata ta fara wata 'yar ƙaramar sana'a. Wani ɓangare ne a cikin ɗakinta ya zama kamar kanti wanda take zuba kayan da take sayarwa, saboda ba ta da wani shago.

**Bayanin Aminata cikin Faransanci:**

*"To, a nan nakan ajiye takalman da nake ba wa mutane bashi. Ban da wannan ina yin wasu abubuwan da suke kawo mini ɗari da kwabo: ina sayar da kayan ƙwalam da maƙulashe, irin abubuwan da yara suke so kamar su ƙosai da fanke. A ƙarshe kuma nakan lissafa na ga ɗan abin da na samu na kuma ware wanda zan ajiye."*

**Mai ba da labari:**

Ga 'ya'yan Aminata nan suna wasa da na maƙwabciyarta Hélène a tsakar gida. Hélène na zaune gida ɗaya da Aminata. Duk da cewa shekarunta talatin da kaɗan ne kuma 'ya'yanta biyu, ta ce ta damu da irin rayuwar da 'yan'uwanta matan da aka mutu aka bari suke yi. Ba wani taimakon kuɗi da za ta iya ba su, amma tana ƙoƙarin taimakawa da shawarwari, tana kuma kusantarsu.

**Bayanin Hélène cikin Wolof:**

*"Ina ganin ya zama wajibi mu taimaka wa irin waɗannan matan. Da ina da iko da na taimaka musu. Ba kuma matan da aka mutu aka bari ba kawai, ya kamata mu tuna da matan da mazansu suka gudu suka bar su ma."*

**Mai ba da labari:**

Ba ita kaɗai ba ce take da wannan tunanin ba. Mamadou Dabo malamin makaranta ne, yana kuma zaune ne a unguwa ɗaya da Aminata. Shi ma yana kira da a ƙara taimakawa da kuma kula da matan da aka mutu aka bari. Yana jin tausayin irin waɗannan matan sosai.

**Bayanin Mamadou Dabo cikin Farasanci:**

*"Ya kamata a yi doka a majalisar ƙasa a kan yanayin da waɗannan mata suke ciki, waɗanda wani lokacin ake yin watsi da su."*

**Mai ba da labari:**

Abin takaicin shi ne ba dukkan maza ne suke da wannan ra'ayin ba. Wani lokaci akan ƙyamaci matan da aka mutu aka bari, a kuma nuna musu bambanci. Waɗansu mazajen suna ganin mata ne suka jawo wa mazajensu bala'in da ya same su. Wannan shi ya sa yake da wuya ga matan da aka mutu aka bari su sake yin aure. Kashi 95 cikin ɗari na mutanen Senegal Musulmi ne. Shin irin wannan halin nuna ƙyamar yana da dangantaka da addini?
Idrissa Konaté malamin addinin Musulunci ne. Kamar yadda ya yi bayani ba wani dalili da zai sa a ƙi aurar matan da aka mutu aka bari. Dalili shi ne, Annabi Muhammadu (SAW), wanda shi ne abin koyi ga dukkan Musulmi, ya auri matan da aka mutu aka bari.

**Bayanin Idrissa Konate cikin Faransanci:**

*"Bai kamata a ce ina koyi da Annabi Muhammadu ba (SAW), sannan a ce na ƙi auren matar da aka mutu aka bari ba, ba zai yiwu ba. Amma akwai mutanen da suke da wannan tunanin."*

**Mai ba da labari:**

Kamar yadda Idrissa Konaté ya yi bayani, irin waɗannan mutanen sun yi imani cewa idan mijin mace na farko ya mutu, na biyu ko ma na uku su ma suka mutu, to na gaba shi ma mutuwa zai yi.

A ƙi aurar mace wai don mijinta na baya mutuwa ya yi, shi ma wani nau'i ne na nuna ƙyama. To amma fa auren nasu wani lokacin ma yana zama mara amfani domin kuwa akwai mazan da suka ɗauki irin waɗannan mata ababan ɗanɗanawa kawai. Aliou Fofana wani masanin kimiyyar zamantakewar al'umma ne wanda kuma ya ƙware a kan harkokin da suka shafi tsarin zamantakewar iyali, ya ba mu misalin wata matashiya da mijinta ya mutu, wadda kuma mazan da ta je neman taimako wajensu suka nemi su yi lalata da ita.

**Bayanin Aliou Fofana:**

*"Ta dogara ne da taimakon da take samu daga wajen mutane don ta ciyar da 'ya'yanta. Waɗansu mutanen sun fahimci halin da take ciki kuma suna taimaka mata, amma waɗansu sai suke amfani da wannan damar suna cutar da ita."*

**Mai ba da labari:**

Bugu da ƙari wani abin takaicin shi ne, wani lokacin danginsu ma kan yi watsi da su. Kanwar Aminata da ta surukanta ba ta juƙuwa ƙwarya ɗaya saboda ganin yadda ta bar gidan mijin nata ba ta faɗa musu ba. Yayin da yake da rai kuwa duk a gidan iyayensa suke zaune.

**Bayanin Aminata cikin Faransanci:**

"*Kafin ya yi aure yana taimaka wa 'yan'uwansa. Amma taimakon sai ya gagara bayan ya yi aure saboda nauyina da na 'ya'yana ya hau kansa. Su 'yan'uwan nasa ba su yi masa uzuri a kan haka ba, sai suka dinga cewa ya tare a wajena."*

**Mai ba da labari:**

Akwai jan aiki kafin a kawo ƙarshen nuna bambancin da ake yi wa matan da

mazajensu suka mutu. Ita Aminata kuma tana son ta taimaka don hakan ta samu. Babban burinta shi ne wata rana ta kafa wata ƙungiya ta mata matasan da aka mutu aka bari ta ’yan kasar Senegal.

**Mai gabatarwa:**

To, da wannan hasashe na wannan matashiyar mata da aka mutu aka bari, wato Aminata, muka kawo ƙarshen wannan kashi na “Ji Ka Karu”. Wanda ya haɗa mana wannan rahoto shi ne Babou Diallo wanda wani ɓangare ne daga cikin shirin da muke kawo muku na musamman a kan mutunta haƙƙin tsirarru.

Idan kuna muradin sake sauraron wannan shirin da ma wasu da suka gabata, sai ku ziyarci adireshinmu na yanar gizo, wato dw.de/lbe. Kazalika za ku iya tofa albarkacin bakinku a shafinmu na ‘Facebook’. Sai mun sake saduwa!